Nasmat dataki yin shiru tace dad inada question dayawa.... Kuma kamun promise indan naji sauki zaka amsa mun ko kai yada mata.... Yace to kiyi shiru ko....... Kizauna da antynki barin Kai mom gida kafin ayi salmah ko.... Gyada me kai tayi dan nasmat akwai shagwaba...... Suna fita ba wanda yace ma wani ufan acikin su.... Salmah na tunanin jalal..me yadawo dashi cikin rayuwar ta bayan ta shafe babin shi.... Ita kuma nasmat na tunanin rayuwar su... Yadda zata kare da bakin painting da mom ta musu... ...

Salmah tayi nisa cikin tunanin ta tace Anty salmah dan Allah kiyi hakuri kinji..... Daga mata hannu kawai tayi... Nasmat saukowa tayi kasa inda antynta ke zaune tayi kneeling tace pls my Anty am sorry for the disrespect... Tace is OK... Rungume tayi sukayi ta kuka.... Can nasmat tace anty dan Allah waye.... JALAL.......

Typing......
By:H.@.S🔴🔵
[3/1, 12:26 PM] H.@.S🌺🌸: 🔵🔴🔵🔴🔵🔴🔵
🔵🔴🔵🔴🔵
🔵🔴🔵
🔵

AUREN JINSI.

🔴🔵🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴
🔴

28-2-2018

Typing.... 76 to 80

Dedicated: HANAN ABUJA.

Gaskiya yar uwa nagode da abun arziki... Yaba kyauta tukuici ne... Allah ma yace indan yabaka ka gode masa sai yakara ma.... Indan kuma ka kafurce to lallai ya tanadi azaba me tsananin..... Hanan naji dadi kuma nagode.... Allah yabar zumunci yaraya miki zuri'arki.... Yakareki daga sharrin masu Shari.... Allah yasaka da alkhairi...🤝🤝🤝🤝🤝🤝🤝

Hajiya kema sakonki ya iso gareni... Nikam ba abinda zance sai fatan alkhairi... Allah yasaka miki da alkhairi... Allah ya raya miki iyalanki.... Allah kuma yabar ki... Da me house.... A

dade anayi sai gaskiya....🤝🤝🤝

Fans kuma naji dadin yadda kuka mun jiya gaskiya ba abinda Zan iya cewa sai Alhmadulillah..... Nagode sosai.... MARWANATU..... ina ji dake kema nagode da kuwalarki.. yabaki abinda kike nema duniya da lahira......

🔴🔵HOME OF MY QALAM WRITER'S ASSO🔵🔴.

Ku kasance tare da alkalamina.... Dan fadakarwa , illimatarwa.... Game da nisadantarwa.... Daga yar mutan jasawa....
🔵🔴🔵🔴

Tace anty waye.... JALAL .... Gaban salmah ne yafadi.... Amma ta dake tace a ina Kika samu sunan jalal... Kuma.... Ban San ko waye ba... Tace Anty nasan bakya karya... Amma yau kina so kifara kenan..... Naji kuna waya dad ranar.... Kuma wayar na hands free take.... Naji me kike cewa.... Dan Allah I want to know little about him.... Nasanki da kamal ba jalal ba... Amma duk lokacin da zakiji wani Abu gameda... Jalal zuciyarki na rawa idanunki na fitar da ruwa.... Dazu nasan dashi kuka yi waya... Tunda naga har kin kashe waya kuma bakya marmarin... Kara kunnata........ So pls Anty..... Tell me something about him..

Salmah guntu hawaye ta goge.... Tana mugun tausayin kanwarta... Allah yarabaki da kadarra irin ta wa....zaunar da ita tayi kusa da ita... Tace Zan baki labarin jalal amma...abisa sharadi daya.... Dan naga alama nasmat acikin hayyacinki kike ....dan duk wanda zai iya wadannan tamboyoyi to nidai aguna lafiyar shi kalau.... Dad ma ya biye miki saboda shagwabar ki.... Amma nifa bazan iya ganin kina muzanta mun mahaifiya ba bazan dauko ba... Ga dukkan alamu kin dade da yin watsi da ita a matsayinta na mahaifiya ba.... So what ever... Kome kika ji Kika ganin tare da ita kisani ita mahaifiyar ki ce... Kuma ita ce sila data kawo ki duniya....

.....safiya dake sunan mahaifiyar Alhaji gareta..... Kisani duk duniya zaki iya canja komi amma fa banda iyaye.... Kuma zaki iya siyan komi amma banda iyaye domin kuwa basu da kasuwa..... Ina so kisani.... Iyaye amana Allah yabasu zai tambaye su game da Mu muma kuma zai tambaye Mu akansu..... Kinga kowane sashi an bashi amana...... Allah yana cewa kulkum rã'ee wa kullkum mãsul.....dukkan mu kiwo aka bamu ....kuma zamu kasance abbaben tambaya...... Allah yana cewa a cikin alqur'an me girma..... Adi'ulllaha wa'adiul rasullu... Wa aullu illim minkum..... Nasmat kina da saninki iya gwargwado.... Amma kina nema ki jefa kanki cikin halaka......

Lallai nasan kome Kika ji nasan babban ne ....kuma bana fatan jinshi..... Amma ai kamar yadda iyaye nmu suke indan munyi Abu ba daidai ba... Suke mana fada haka muma indan sunyi ba daidai ba.... Zaki iya afani da wata siga ko dubara da Allah yabaki.... Wajen musu nasiha.... Da kuma nuna musu kuskure.... Amma ba saikiyin fushi da su ba ko kin muzanta su.... Wanda Allah yagaya mana yadda zamu zauna dasu.... Yace kar da muce musu tir... Kuma kada Mu hantare su Mu gaya musu magana me daraja..... Amma ke kin take saninki kin bi rudin shedan...... Nasmat ba wai na zaunar dake bane dan namiki dadin baki ki janye gudurinki aa.... Sai dai ina tuna miki fushin Allah akanki ne......wanda Allah ya tanadi azaba Kala Kala.... Akan masu. Kinyi ma iyaye azaba.... Kuma tunda ga duniya baza su ga abinda suke nema daidai ba..... Kamar yadda nace miki Zan baki labarin jalal.... Sai kin mun alkwari bazaki kara kallon banza wa mom ba.... Kuma bazaki kara mummunan magana akanta ba...... Idan har kin mun wannnan alkwari to.... Ki miko mun hannunki......

Nasmat ta dade a durkushe tana kuka saboda kalar nasihar da nasmat ta mata gabadaya jikinta yayi sanyi.... Duk abinda salmah ta fada gaskiya.... Amma abun mom din nasu da yayi muni amma zatayi iya kokarinta...Wajen dagewa da adu'a Allah yaraba mom da wannan hali tun kafin dad din su yasan abinda ake ciki....... Mikawa salmah hannunta tayi.... Suka rungume juna..... Suna kuka salmah ta dago ta.... Ta share mata hawaye itama nasmat ta share ma salmah hawaye.... Tace antyna in Allah ya yadda na daina.... Zan cigaba da adu'a Allah ya sautata mun wannan Abu aciki raina.... Amma antyna mom na bukatar adu'armu sosai.... Abun yayi muni dan Allah Anty kidinga sata a adu'a kinji.......

Tace naji kema ki dinga adu'a kuma indan mun koma gida kije kinemi yafiyarta.... Kinji gyada mata kai tayi tace insha Allah zan aikata.......

Miqad bayan ya huta.... Ne dan tunanin salmah ya hanshi sakat.... Tunda yadawo yake tunaninta ganin jarabarta kawai yakeyi yana murmushi..... Yace nayi mata insha Allah.... Wanka shi yasha cikin manya kaya idan ka ganshi sai ka rantse ango ne... Iya haduwa ya hadu.... Gun mahaifiyar shi yaje cikin annashuwa ....tace bunnaya illa aina tazhabul min hazal... Har..... Dariya yayi yace Ummi na balarabiyya..... Kimun adu'a Ummi.... Tace kullum acikin ma ita nakeyi.... Allah yamaka albarka.... Kaji dana.... Yace ummina wannan adu'ar ta musamman ce.... Ta Neman dace ne.... Tace bunnaya kayi isthakar kuwa yace ai dole Ummi.... Sha'anin Neman aure..... Baisan. Sanda maganar ta kubce mai ba.,.. Dan shi yafi so komi ya kankama tukunnah......tace Alhamudillah Masha Allah..... Allah yatabbatar mun da alkhairi..... Kace abun nema yasamu..... Mikewa yayi yatafi.... Cike da farinciki.... Kamar ya riga ya dace ne.....

Basu da nisa sosai dan haka a hankali yake tukin shi.... Kira'ar Ahmad sulaiman na tashi..... Har ya iso abun shi.... Dake ya nuna card din da aka bashi direct gidan yashiga yayi fakin....... Gate man ne yasanar da Alhaji cewa akwai bako........ Sai da gaban Hajiya yafadi dataji cewa salmah ake nema....... A fusace tace kaje kace bata nan..... Dad yace yi tafiyar ka Mallam haliru kace ina zuwa ko...... Haka ake tarbar bako....... Agidana.... Hajiya kamar ta mutu indan yanxu akwai abinda bata so bai wuce ace ana son salmah ba......

Typing.......

By:H.@.S🔵🔴

[3/3, 2:54 PM] H.@.S🌺🌸: 🔵🔴🔵🔴🔵🔴🔵

🔵🔴🔵🔴🔵
🔵🔴🔵
🔵

AUREN JINSI

🔴🔵🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴
🔴

4-3-2018

Typing.... 81 to 85

Dedicated :to my brother....

So fans kun jini shiru jiya hakan yasamo asali ne da rashin lafiyar kanina... Yana hospital a kwance duk wanda yasamu page dinan dan Allah yatayamu addu'a.... Nagode

Kuma nagode wadanda kuka kira kuka ji dadlli....

🔵🔴home of my qalam writer's also. 🔴🔵

Yana daya daga cikin dalilan data sa aka turo salmat karatu waje... Salmah Sam bata da ra'ayin karatu a waje haka shima dadynsu... Shi yafiso yaranshi suyi karatu agaban shi saboda gudun lalacewar tarbiyya a wannan zamani.... Cikin kwarewa Mom tasa Alhaji ya turo salmah karatu waje cewar hajiya hankalinta yafi kwanciya... Kuma ta manta da abinda yafaru da ita..... Dad na yamike ya aje Spoon din hannun shi yace hajiya ta yakike so ayi ne duk sanda salmah zatayi bako tun bayan kamal sai Kin nuna ranki bayaso.... Nasan kina tunanin abinda yafaru abaya ne... Wanda duk wanda ya tuna irin cin fuska da akayi mana zai ji ba dadi amma kisani

ba duka aka taru aka zama daya ba kowa da irin fahimtar sa ko kina so mu dafa salmah mucinyeta.... Ko uba na auran yar shi ne.... Ko kuma da bakya so wani ya zo gunta ke zaki aureta ne intambayeki?

Mom kam da zata iya Bada amsar tambayar nan da taji dadi.... Tace haka bazai yuyu ba amma ina me tabbatar ma abinda yafaru jiya to shi zai faru yau... Kuma duk wanda yace baya sonka da safe.... Dan Da rana yazo yace yana sonka karya ne.... Amma bana fatan bara ta dawo bana ina jiyewa salmah.... Dad kafadar mom yadafa yace insha Allah yata bazata kara dandana irin bakinciki datayi abaya.... Kuma ina ma yara nan kyakyawar fahimta dukkansu ban ware ko daya acikin su ba..... Salmah mutum daya zata Aura... Dan haka bazan hana kowa neman auren salmah ba... Mutakar na yadda da addininsa da kuma Dani'unsa.... Ki kwantar da hankalnki kiyi wa yayanki addu'a dafatan alkhairi.... Bakin ganin ko nasmat ta isa aure ba ma salmah ba... To me zakiyi dasu dukka acikin gida...... Bayan Allah yace indan Sun kai lokaci hakkin mu ne muyi musu aure.... So dan Allah ki janye kudirinki.... Ki tayani lallamin salmah.... Barinje in salami bako..... Mom kamar tayi kuka saboda wani kululun bakinciki ne yatokare ta.... Kwana biyun da salmah tayi kullum da tunaninta take kwana .......

Dad gun miqdad yaje a masaukin baki... Miqad yana ganin shi yace sannu abba... Yana dukar da kai yace abba ina yini.. Abba murmushi yayi yace Ify dana.... Ya rana ya kuma hutu yace alhmdlh.... Dad zama yayi yace miqdad nasan salmah kazo nema ko.... Ya Asma mai da A amma kanshi na kasa.... Dama kasamu wani information akanta yace no. Abba amma dai tace mun ita matar aure ce.... Shiyasa yau nazo inji gaskiyar maganar..... Abba murmushi yayi saboda agidar da salmah ta dasama zuciyarta yafara tasiri..... Yace salmah ba matar aure ba ce...... Amma Kuma amatsayin datake yanzu kusan a haka take..... Ido miqdad ya zaro dan yafirgita sosai ....Dad yace kwantar da hankalinka dana.... Salmah ta gidaya ma kanta wani shardi na bazata kara saurayi ba saboda wani irin kalubale data fuskanta.... So ni abu daya zan gayama ni bazan ma yata auren dole ba.... Kayi kokari ka Nemo soyyayar salmah da hannunka...... Ita mutum ce me saukin kai.... Amma zaka gani da idonka.... Amma yanzu bata nan tana gun yar uwarta a hospital.... Miqdad ba karamin dadi yaji ba saboda shi duk wani wasu steps da suka rage ganin su yakeyi Sun fi komi sauki..... Yace Dad dan Allah ka taimake ni da contact dinta.... Dad baiyi musu ba yabashi dan yasan waye family margayi..... Kuma zai so ya hada zuri'ar shi da wannan babban family.... Yace Dad amma wani hospital ne yace karka damu yau insha za'ayi discharged nata..........

A hospital kuwa da salmah da nasmat hirar su sukeyi cikin nishadi da fahimta da kuma kulawa da shakuwa irin na yan uwantaka..... Tace Anty ranar da mukayi waya dake nake ce miki yaushe zaki fito da miji musha biki.... Sai naji muryarki ta shake kamar zakiyi kuka...... Salmah tace saboda ni banda saurayi Kuma bana so ma nayi..... Saboda ni bana she'awar auren yanzu..... Kin gane sis yanzu ba lalle ki fahimci ni ba amma indan nabaki Ibr waye jalal da Kuma kamal zaki tayani yanke hukunci game da soyyya.... Tace to Anty kira Dad yazo ya maida mu gida..... Tunda anyi discharge dina..... Kunawa tayi.... Taga sako sunata shigowa.... Bata dade ba wayar tafara ringing..... Kin dauko tayi wata number ce still ta shigo an rubuta My childhood frnd.... Dariya tayi ta dauka....daga dayan bangaren akace ke kullum sai Kin ja aji ne before picking ne.... So yakike so ayi.... Wama yagaya miki nashigo 9ja me........ Hmmmm mutane mana..... Akwai News ne.... Sai nazo ina little din mu ne.... Tace itace ma bata da lafiya..... Subhallah meya sameta.... Ke fever ne kawai tasamu sauki ma...... Ok Allah yabata lfy.... Amin

Ina baby mu da kuma oga..... Duk lafiya.... Waike frnd sai yaushe zamu sha bikine.... Tace yanzu mana.... Kin fiye wasa dayawa... Pls keep juck aside...... Wai ina jalal ne..... Tsaki ta ja ta kashe wayar.... Mutum bazai taba zama lfy ba batare da an bata me rai ba..... Ke ungo kira Dad din barin hada kaya kinji.........

Nasmat na searching contact din Dad hannunta ya janyo wani text ya bude..... Karantawa takeyi..... A hankali taga ansa dan Allah ki taimake ni ki aure ni...... Ni macece amma zan iya biya miki bukatarki wallahi komi yawan bukatarki dan Allah ki fahmce ni..... Ni me sonki ce....... Sallati nasmat ta kurma..... Salmah ce ta juyo dan ganin abinda ke faruwa..... Ganin nasmat na kallon waya kuma tana sallati tana hawaye yasata karasaw gun...... Mezata ganin

Typing.....

By:H.@.S🔵🔴

[3/4, 2:15 PM] H.@.S🌺🌸: 🔵🔴🔵🔴🔵🔴🔵

🔵🔴🔵🔴🔵

🔵🔴🔵

🔵

AUREN JINSI

🔴🔵🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴
🔴

4-3-2018

Typing..... 86 to 90

الحمداللہ الحمداللہ الحمداللہ..

Dukkan godiya tabbata ga Allah.... Yan uwa nagode muku sosai da sosai... Abisa kira na da kuka dinga mun da wadanda suka mun text nagode Allah yabar zumunci kuma me jiki alhmdlh jiki da sauki....

Bammali ce kema nagode da irin taki kulawar..... Maman pharteemah daga group na khaleesat hydar novel nagode sosai.....
Mimsqueen kema nagode kawar albarka....
Hanan kema nagode da jajantawa.....
Aysha Muhammad kema nagode.... Kuna dayawa bazaku lisafu ba.....

Taka daban ce bros... Ibrahim kaima ka bada irin taka gudumarwa ko yaushe kana bibiyar novel dinan.... Nagode.....

🔵🔴HOME Of My QALAM WRITER'S ASSO. 🔴🔵

jikinta ne ya hau rawa.... Da sauri ta karbi wayar tace a ina kika janyo wannan text din cikin rudewa nasmat tace ina kanyi searching cikin contact din Dad ne hannuna ya taba saman screen shine text din ya bude shine kuma ki ka tsaya karantawa ko saboda naki ne..... Tace

Anty ki karanta mana kiji me text din ke nufi wallahi masifa ne..... Amma Kuma ta private number ne.... To ina ruwanki da karanta abinda bai shafe ki ba.... Nasmat bazaki gane masifar dake tare da wannan text din ba daga yau sai yau bana so ki sake maimaita mun irin wannan mistake kinji tana murda mata kunne..... Salmah cikin tashin hankali take maganar da kuma idonta daya kada yayi ja dialing number Dad din tayi tace mun gama Dad....... Ok kawai tace.... Tasamu gu ta zauna tana tunanin ita dai yanzu ba saurayi tayi ba ballatana tace kuma za'a kara tarwatsa ta.... So tadaina soyyayar ma amma bata tsira ba gashi duk abinda take boyewa nasmat na kokarin tono shi..... Tasan lallai sai ta fahmci wani abu amma ita ba wannan damuwarta ba..... Waye me mata wannan dayan aiki..... Nasmat tun dazu bata matsa daga inda take ba tace nashiga ukuna ni safiyya ya zanyi da rayuwata.... Ashe dama Dabi'ar mom da salmah iri daya ne... Itama mata yan uwanta suna nemanta kamar yadda mom ke neman jinsi ta dan ganin tasamu biyan bukatar ta..... Ashe shiyasa salmah take mata WA'azi domin itama tasan tanayi.... To wallahi sam bazan iya zama da masu sabon Allah..... Al dama berawa bazatayi gudu ba danta yayi rarrafe ba.... Sai Allah yasakawa ya'yan mutane da momy ta lalata..... Hawaye ta share tace dadynmu Allah yabaka hakuri akan jarabawa daya dora ma Allah yabaka ikon hakuri akan irin abubuwa da iyalanka ke aikatawa.... Dad ban san wani irin Acton zaka dauka ba duk ranar da kaji ko ka ga abinda nagani ko naji..... Maganar xucice tafito fili.... Salmah ce ta matso kusa da ita tace sis kar ki yanke hukunci acikin duhu Kuma kar ki dorar da abinda Bakida tabbas dashi kiyi bincike kafin aiwatar da komi...... Bige mata hannun tayi tace kar kisake tabani da wannan kazamin hannun naki Kuma bazan kara yadda da zance ki ba..... Kuma ke ba yar uwata bace......... Salmah bakin nasmat ta bige tace ke yar iska ce ko.... Wai yaushe kika girma ne har Kin iya yiwa mutane futsara...... Tace ke ce babbar yar iska.... Kuma wallahi kika kara kirana da yar iska sai Kin....gane shayi ruwa..... Salmah dauke fuskar tayi da mari..... Zata kara marinta ne yayi daidai da shigowar dad ya rike sallama...... Ya wanke ta da mari yace ashe Kin maidani mutum banza ko tunda ban isa ingaya miki ba..... Kuma wallahi daga yau kika sake kika kara tabata duk hakuri na saina nuna miki kuskurenki.... Shasha kawai dama nabarki a hospital ne dan kiyi treating dinta yadda kike so.......

Nasmat ya kamo da fuskar nan tayi ja duk shattin yatsun salmah... Yace sorry My daughter tashi ki shirya in maida ku gida kinji kiyi hakuri kinji bazata kara tabaki ba indai akan ciwonki ne....... Tace Dad wallahi indai motar da salmah zata shiga ne to nidai sai dai in tari abun hawa dan bazan taba shiga mota daya da ita ba...... Dad yace yi hakuri dan shi ganin yake ciwo ke sata wadannan abubuwa dan haka yake lallabata..... Salmah kam kuka tashashi....Dan haka ta dauki hand bag dinta tayi waje tabar Dad da nasmat a ciki.... Tunda taga taketaken nasmat....... Tana fita harabar asibiti taci karo da miqdad zai shigo cikin hospital din rike da leda..... Yace antymu ina zuwa haka.... Bangaje shi tayi tsaki..... Binta yayi yace inkina kaunar Allah da manzon sa kuma kina kaunar iyayenki ki tsaya ki gayamun Ward din da suke.... Cak ta tsaya murmushi yayi yace I got one...... Kusa da ita ya mtsa yace antymu ai komi yayi zafi to maganin shi Allah ki yi hakuri da kaddara me kyau da kuma mara kyau..... Mika mai wata

ta kadda tayi dan bazata iya magana a wannan lokacin ba..... Dubawa yayi yaga sunan Ward din ta rubuta... Gaba tayi abinta dan bata mata waye shi ba.... Yaci darajar Allah ne kawai ta tsaya karasawa ysyi ciki... Yaga su Dad har Sun fito..... Gaishe shi nasmat tayi yamata yaji..... Dad yace har an salleme mu ....baka hadu da mutuniyarka bane yace a nagsnta..... To barin sallami doctor sai mutafi.....

Salmah tunda tsfito tske taran abun hawa amma babu.... Ta dade har dady yazo ya wuce da nasmat a motor bai kula taba ya wuce akan zaije yadawo ya lallasheta..... Yasan bazata samu abun hawa ba..... Miqdad ne shima yafito dan tsfiya ya ganta zuge glass yayi yace antymu baki tafi ba ashe batayi magana ba.... Yace kin san nan ba asamun abun hawa.... Indan wani gu zaki muje in aje ki..... Bata kulashi ba still..... She ko bai son ganinta acikin rana ga kuma zafi..... Kuma tana cikin tashin hankali..... Fitowa yayi yace dan Allah ki shiga mu wuce kinji..... Kamar gunki haka take tsugunawa yayi yace dan Allah kishiga...... Tsawa ta daka me tace wani irin iskanci wai wannan..... Zaka kara ja mun wani zagi ne..... Ka tashi ka tafi bana son taimakonka..... Na Allah nake so.... So kawai ka tafi..... Yace indan kin ga nabar nan kin shiga motar ne so zafi ya rage naki....... A hankali mutane ke taruwa dan kallon meke faruwa...... Wasu Sun zata mata da miji ne...... Ma saboda sunyi Bala'e'en match da juna........ Wata budurwa ce ta karaso tace baiwar Allah ai kome ya miki haka ke bari .......

🔵🔴🔵🔴
[3/5, 11:03 AM] H.@.S🌺🌸: 🔵🔴🔵🔴🔵🔴🔵
🔵🔴🔵🔴🔵
🔵🔴🔵
🔵

AUREN JINSI

🔴🔵🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴🔵🔴
🔴🔵🔴
🔴

5-3-2018

Typing...... 91 to 95

Dedicated: to my mom and dad.....Allah yakarawa rayuwarku Albarka... Allah yajikanku badan kun mutum ba...

Hafsat Abdullahi shu'aib lovely sis.... Wallahi Ina sonku sosai.... Baki bashida Kalmar godiya agareki..... Ina fatan kina Ify ...ya zafin Cameron.... Ina my Cherie saeema kema fa ina yinki irin totally din nan...

🔵🔴HOME OF MY QALAM WRITER'S ASSO.🔵🔴

Tace baiwar Allah ai ko me ya miki haka ke bari kuje gida ko.... Amma ki dinga tozarta miji agaban jama'a haka.... Manyan idanunta ta daga ta watsa mata harara..... Tace angaya miki kuma miji na ne ko..... Mutane kun fiye shishigi dayawa.... Dadina da kasar waje kenan ko me aka ga mutum nayi bara su saima idon ba.... Amma dubi yanzu har an wani cika gu....... Kai kuma wallahi indan baka tashi ba wallahi sai na cire takalmina na kwada ma a a goshi..... Tun baka jamun zagi ba... Kuma kaji da kyau wallahi tallahi bazan shiga motor ka ba ko dole ne wai..... tunda miqdad yaji tayi rantsuwa yace a lallai da gaske takeyi mikewa yayi daga tsuguno ya bude motor shi ya ciro lema ya mika mata yace tunda kin rantse baran Saki dole ba amma dan Allah ga lema ki kare wannan ranar..... Karba tayi ta kwada masa akai.... Tace baka da hankali ne ko Zan koya ma.... Ko zanyi soyyaya bazan yi da irin ka ba..... Saboda shiru tayi lokacin data ga jinin na malala daga kan shi yasa hannu ya dafe gun.... Duk junin ya wanke me fuska... Ga farar shada shi duk ta baci..... Mutane ke magana akan rashin imani da kuma tausayi.... Suna ta tir da halin salmah... Jikinta ne yayi sanyi sosai.... Dan wallahi batayi tunanin zata jimai ciwo ba.... Kuma ita din ce sai a hankali domin ranta duk ya baci..... Matsawa kusa dashi tayi ta dora hannunta agun ciwo... Tace muje cikin hospital a ma dressing din gun.... Shiyasa ban nason yawan naci..... Hand chief ta dauko ta Dora agun ciwo... Gaba tayi yabita a baya.... Shi kam dadi yaji domin yanzu ya gano wanin abu a tatare da ita.... Sai da ta jira aka gama me dressing sannan ta fito...... Tana fitowa dad nadawo wa.... Yace yar baba ina Kika shiga ne.... Inata jiranki haka ina shirin dialing number ki kenan fa.... Baki ta zunbura tayi gaba abinta..... Da da yadda zatayi bazata shigar motor dad ba amma yanzu bata da zabi bude motor tayi ta shiga.... Miqdad ne yafito kai duk bandage... Dad ya kalli shi.... Yace badai salmah bace tama wannan aikin haka ko..... Tana motor tana kallon bakin miqdad dan Karami dashi.... Taji me zaice.... Dan inya ce itace to wallahi ta shiga uku....

No dad na fito daga cikin hospital ne sai nazame na fadi.... Salmah ce ma taimaka mun aka gyara gun.... Dad dai bai yadda ba yasan yadda yabar salmah dazu to zatayi fiye da haka ma..... Allah yakiyaye nagaba dad yace.... Allah kuma yabaka lafiya... Kaji..... Kowa motar shi yashiga ..dad dayafara tuki yace salmah me bawan Allah ce yamiki Kika mai wancan aiki..... Ido ta kwalalo ta ce nikuma me yahada ni dashi da Zan me wannan aikin haka..... Nima na koma cikin ne dan ban samu motar ba na ganshi a wannan yanayi shine fa nataimake shi..... Dad tamke fuska yayi yace salmah yaushe kika zama yar ta'ada ne ban sani ba..... Kin San duk dabi'unki sun canja ko.... Duba da yar uwarki salmah kin San halin data ke ciki... Amma daga barinki a hospital kin meda musu hospital gurin dambe.... Haka babba yakeyi indan yana gu gaskiya ban ji dadin abinda kika yi ba....... Ni danake fata yanxu indan bana raye ke kizama me kula da mahaifiyarki da kanwar ki..... Haba salmah shifa mutum kullum in yana girma dabi'unsa kyau suke karawa..... Ni Allah bai ban ya'ya masu yawa ba ba kuma bana so bane aa sai dai kawai haka Allah ya rubuta mun..... Ina muku adu'a Allah ya shirya Ku.... Ke kadai salmah indan Allah yaba mutum zaki isashi rayuwa har abada..... Toni me xance ma Allah banda godiya yabani yaya har guda biyu........ Salmah dazu bana fifita nasmat akanki bane sai dai kawai ina so nazama uba me adalci........ Salmah dake kuka tace dad kayi hakuri insha Allah baza'a Kara maimaitawa ba kuma nama alkwari har inbar gari nan baza ka kara ganin nayi ba daidai ba........ Yace meye kuma abun kuka.... Salmah game da bawan Allah nan kuma na dazu.... Salmah bazan tilstaki akan Abu ba amma kisani ita rayuwar ya mace kamar gidan kasa ne shi gidan laka gyara yake so indan baza'a dinka gyara shi ba watarana za'a zo aga. ya rushe... Duk abinda zakiyi kidinga tunanin. ba kowa ake wulakantawa ba a zauna lafiya yanzu abinda kikayi kiyi daidai... Kenan.....wannan yaron da ban yadda da tarbiyyarshi bazan amince dashi ba.... Amma bazan cunkusa miki ra'ayi akan abinda baki dashi ba amma a matsayinki na me hankali ina baki shawara akan wannan yaro nida na amince dashi indan Allah yasa kin amince da shawarata salmah ki amince dashi......

Yanata mata nasiha har suka iso gida..... Yace share hawaye nan bana so kishiga dasu.... Gogewa tayi... Tashiga gida.... Dakinsu ta wuce direct.... Turo kofa tayi hade da salmah amma ko ajikin nasmat bata motsa ba ballatana tasan sallama akeyi.... Maimaitawa salmah tayi.... Ciki ciki ta amsa..... Salmah ta shigo tace sis kenan da baki amsa ba ma mala'iku zasu amsa..... Nasmat da kamar bata jin abinda ake fada tace suma mala'iku salamar mutane arziki suke amsawa ai...... Kamar ba ita tayi maganar ba ta koma ta lumshe ido..... Salmah kallonta tayi da mamaki me kalaman nasmat ke nufi..... Watsar da tunanin tayi ta shiga bayi abunta wanka tayi tafito tasa doguwar riga.... Zatayi sallah.... Hijjab din nasmat ta dauko a bakin kofa.... Nasmat bude ido tayi tar akan salmah da hijjab dinta..... Mikewa tayi cike da azama ta fisge hijjab dinta.... Tace mallama kar ki kara samun hijab.... Ballatana kisa mun najasa..... Ki nemo naki....

Wannan ma bazan Kara sallah dashi ba.... Domin Allah me tsarki ne kuma baya karban wani aiki sai me tsarki dan haka akiyaye taba mun suturata ko........ Salmah sandarewa tayi..... Lallai me yarinyar nan ke nufi da ita..... Badan alkwari datayi da dad dainsu ba ba abinda zai hanata cima nasmat uwa agidan nan..... Trolley dinta ta janyo ta bude ta dauko kayan sallanta........ Salmah na sallah nasmat na tunanin ta tana kallon salmah dan Allah dubeta kamar wata muniyar kirki....... Mu dai Allah yahada mu da jarababbun.... Allah kuma yashirye Ku......

Typing.....

By:H.@.S🔵🔴

[3/5, 6:59 PM] H.@.S🌺🌸: 🔵🔴🔵🔴🔵🔴🔵

🔵🔴🔵🔴🔵

🔵🔴🔵

🔵

AUREN JINSI

🔴🔵🔴🔵🔴🔵🔴

🔴🔵🔴🔵🔴

🔴🔵🔴

🔴

5-3-2018

Typing.... 96 to 100

Dedicated : to u my Ummu jalal.... Can you close your eyes for a minutes please........ thank u.....

Did you feel how dark it was? This is my life without a sweet friend like u.

I may have forgotten to say that I Care. I may have failed to open up and share, but though no words have been spoken, my promise of friendship won't be sis amoon... I like your style.......

Salmah sallah tayi a nitse bayan ta idar ne ta dade tana rokon Allah akan matsalolinta da kuma.... Ciwo Wanda ake cewa nasmat Nada shi.... Dan ta fara yadda da maganar dady su nasmat nada tabin hankali ko kuma aljannu sun taba ta..... Ta dade tana Adu'a..... Nasmat na kallonta.... Tace mutane sai boyyayen hali... Ashe dama halin mom dinmu kika dauko sai dadin baki.... Allah yasa na gano ko suye Ku.....tashi tayi daga kwance datake.... Ta daga hannu sama tace Allah ina rokonka da kyakyawan sunayenka guda Dari ba daya....indan zaman nan danakeyi acikin wadannan mutane alkhairi ne Allah ka tabattar mun da allhairi inda kuma Shari ne agareni da kuma addininka Allah ka kubtar dani daga cikin su... Mikewa tayi zata fita salmah data shafa adu'arta... Ta juyo tace my little ina zaki.... Nasmat bata juyo ba bata kuma tsaya bata kuma yi magana ba..... Salmah tace ki dawo ki zauna muyi magana kinji..... Juyo tayi da gadara tace ke har kin isa ki zaunar dani ne ballatana ki gayamun yaudararun kalamanki ki rike kayanki..... Yanzu ma zanje gun daddy ne ingaya Mai cewa yaraba mana daki.... Dan zama da irinku hatsari ne.... Sai Ku dilmiyar da mutum nan da nan..... Tsaki taja tayi waje.... Salmah kam sai kuka abun ya hadu ga me saurin kuka tace ni salmah kai chona meke shirin faruwa dani ne.... Allah ka kawo mun dauki... Cikin gaggawa.... Zuciyata zata iya fashewa...... Bazan iya daukan kalaman nasmat ba... Sun min nauyi....... Daddy ba karamar kaduwa yayi ba da jin zance nasmat....... Wai yaraba musu daki da salmah... To me yake damun yar shi haka ko menene ma to babba ne duk kusanci da shakuwa dake tsakanin salmah da nasmat da irin soyayyar da suke wa juna gaskiya dole yatashi tsaye dan nema wa yar shi magani..... Kiyi hakuri da yar uwarki nasmat indai akan abinda yahadaku ne dazu to na tabbatar miki bazata kara maimaitawa ba... Dan tamun alkwari...kiyi hakuri nasmat... Ko kina son ganin farinciki ne daga Mai kai tayi alamun A... Yace to kiyi hakuri ki zauna da yar uwarki lafiya.... Nasmat Ku biyu kadai Allah yabani aduniya nasmat indan Baku hada kai ba ya kuke so inyi nasan lalura ce tattare dake.... Tace dad wallahi tallahi lafiyata kalau kawai bana son kasancewa da mutane masu sabon Allah ne.... Dad ina so a rayuwata inyi abinda Allah ya umarce Mu dashi kuma yake so Mu aikata.... Dad Allah yayi hanin da wasu manyan kaba'ire masu girma Wanda yace kar a kusance su ballatana aikata su..... Dad ina da hujja dayawa a hanuna Wanda ko aAgun Allah indan na kauracewa mom da salmah dad banyi laifi ba..... Ina ma adu'a ranar da zaka gano abinda nagano.... In zuciyarka bata tarwatse ba...... Zan cigaba da shiru... Amma dad kayi sakaci da amanar da Allah yabaka..... Dad Abu daya zan rokeka.... Dan Allah yanzu kar ka kuma nisa da iyalanka dad kasa ido sosai akan iyalanka duk ranar dakake bukatar karin bayani

akan abinda idonka yagani ko kunnenka suka ji a shirye nake...... Amma kasani yanzu bazan taba jituwa dasu ba har sai ranar da suka gano gaskiya a tattare su.......

Dad cike da mamaki yake kallon nasmat.... Wai yasa ido akan iyalan shi kuma kar yayi nesa dasu me nasmat ta gano Wanda shi bai gane ba... Me mom da salmah ke aikatawa Wanda nasmat ke tsoron fadawa tarkon su..... Bashida amsar tambaya......? Yace safiyya insha Allah zan kasance tare daku har zuwa lokacin da Hutu na zai kare kuma zansa idon akan lamuranku insha Allah nagode da tunatarwaki amma akwai abubuwa masu dama dasu ka daure mun kai.... Kuma zan nemoki nan bada dadewa ba.... Kishiga ki kira mun mom da salmah duk kuzo tare kinji.... Bai wai ranta yaso bane amma bazata iya tsalleke maganar dad ba....Sashin mom ta nufa... Tana zuwa bakin kofar dakinta ta tuno da abubuwan da suka faru... Jike take kamar yanzu abun ke faruwa... A hankali ta bude kofar.... Ta shiga da sallama idonta a rufe dan ganin take kamar zata ga mom a cikin wannan yanayi ganin ba'a amsa mata sallamah bane yasa ta bude ido ba kowa a daki.... Motsi taji a bayi alamun mom na bayan gida.... Juyawa tayi zata fita taji wayar mom ta dau ruri.... Da kidan su na shahharrun mata... Komawa tayi ta dauki wayar.... Ganin an rubuta me iyali ne.......
. yasata gyara zama a dakin tayi picking..... Batayi magana ba daga daya bangaren akace Hajiya.... Kina magana da Hajiya me iyali ne daga swedan..... To aiki da Kika sani nagama watau nazabo miki kyawawan ehmata har guda uku.... Sai kizaba wace kike so..... Hmmmm Hajiya ai ko muryar su kadai ta isheki biyan bukata..... Amma dai sai kin zo din.... Kina jina kuwa..... Gyaran murya nasmat tayi..... Hajiya me iyali ta cigaba da magana.... Amma Hajiya yarinyar da jiya Kika turo hotonta jiya itama ba karya... Gaskiya mutum zai huta da ita sosai.... Amma naji kince yar ki ce..... Kai shegu mata kuyi dana wasu kuyi dana Ku..... Nasmat kashe wayar tayi da sauri tayi waje..... Dakin su ta koma..... Ta manta abinda aka satayi.... Ji take Allah yasa ba hotonta bane.... Tana shiga taji salmah ma na waya tsaki tayi.... Tace a Abu daya zaku kare ai..... Can karshen gado taje.... Ta bude wayar mom... Katuwar gaske.. Hoton salmah ne akan screen din... Tayi matukar kyau amma itafa yanzu haushi su take ji...... Dannawa tayi tace Allah yasa ba lock a wayar....tana dannawa taga pattern a wayar..... Tunanin ta shiga yi yazatayi ta bude wayar ne...... Salmah data gama waya ta dago tana kallon nasmat da waya a hannunta..... Dubara ce ta fado mata mikewa tayi taje gaban salmah tayi kneeling tace antyna pls harda hada hannu.... Kiyi hakuri kinji.... Da abinda yafaru dan Allah kin iya cire wayar mom a key.... Salmah cewa tayi aa.... Kawai hade da mamaki yarinya yanzu zatayi Abu ta dawo kamar ba ita ba..... Mikewa tayi tace uhm shikenan.... Tayi waje da sauri.....

Typing.......
By:H.@.S🔵🔴